Duk wanda ba ya godewa mutane to ba zai godewa Allah ba

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - daga Annbai - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Duk wanda ba ya godewa mutane to ba zai godewa Allah ba".
[Ingantacce ne] [Abu Daud ne ya ruwaito shi da Kuma Tirmizi da Ahmad]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bada labarin cewa duk wanda a al'adarsa ba ya godewa mutane akan alheri da abu mai kyau da suka yi masa to ba zai godewa Allah ba, hakan dan haduwar al'amura biyun da ɗaya, domin wanda daga cikin ɗabi'arsa da al'adarsa ita ce butulcewa ni'imar mutane da barin gode musu, to al'adarsa zata zama butulcewa ni'imar Allah da kuma kasawa a gode maSa.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/66255